# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na ɗaya: Tsere da gudawa


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Nkoji C. Muhoho |
| Wanda ya tace: | Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Kabir Isa Jikamshi |


**’Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Bilkisu: | ’yar shekara 40 |
| Mariya: | ’yar shekara 43 |
| Hadiza: | ’yar shekara 15 |
| Sama’ila: | ɗan shekara 17 |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da warhaka da kuma sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda a yau zai yi magana ne game da alaƙar tsafta da cutar gudawa. Cutar gudawa ta zama ruwan dare a nahiyarmu ta Afirka, kuma tana ɗaya daga cikin manyan cututtukan da suke yin kisa. A wannan wasa na farko za mu haɗu da Sama'ila da mutanen gidansu, wato ƙanwarsa mai watanni shida da mahaifiyarsa Bilkisu. Amma kuma suna tare da wani abokin zama da ba sa ƙaunarsa, wato cutar gudawa.
Sai a kasance da mu domin jin yadda Sama'ila da 'yan gidansu da kuma abokai suka yi gwagwarmaya da cutar gudawa, domin a san abubuwan da ke haddasa cutar da yin rigakafi kafin a kamu da ita.

**Fitowa ta 1: A filin wasa a makarantar Sama'ila**

Bilkisu, Mariya, Hadiza

**BILKISU** Yauwa Sama'ila, ƙara gudu sosai! Kara gudu, ɗana! Yi gudu!

**HADIZA da MARIYA da BILKISU** …ila! …ila! …ila! …ila! …

**BILKISU** Kai, wancan ɗana ne. Ku duba ku gani! Mariya, Hadiza, dubi! Ɗana Sama'ila yana samun nasara.

**HADIZA** Kai, ga shi kuma ya haɗu.

**MARIYA** Hadiza, ki iya bakinki! 'Yata, kin yi ƙanƙanta ki fara ƙyasa samari fa.

**BILKISU** Hatta ɗana? Na ɗauka aminai ne mu, Mariya!

**HADIZA/MARIYA/BILKISU** …ila! …ila! …ila! …

**BILKISU** Oooo. A'a! Haba, assha!

**CHEMU** Sama'ila, me kake yi haka?

**MARIYA** Aha, ga shi can. Ya kasa jurewa! Kin gani ko Hadiza, rago ne, yaron ba zai iya ba….

| | |
|---|---|
| **BILKISU** | Kai! Dubi, Mariya, ya bauɗe, ya shiga cikin gonarki. Mene ne yake faruwa ne? |
| **MARIYA** | Wancan yaro naki wani bahago ne, Bilkisu. Ta yaya zai bauɗe ya shiga cikin daji, bayan suna daf da yin nasara a wannan gasar tsere mai muhimmanci? |
| **HADIZA** | Me ya faru da Sama'ila haka? |
| **MARIYA** | Tun da kin damu ƙwarai game da abokinki, ki taimaka, ki je ki gano abin da ya sa farat ɗaya ya gigice. Yi sauri, kafin lokaci ya ƙure mana! Yi sauri, Hadiza! |

**MAI BA DA LABARI:**
Idan da kun ga Sama'ila a wata guda da ya gabata, za ku san cewa cin wannan gasa ta tsere tamkar wani wasan yara ne. Amma kuma cikin 'yan makwannin da suka gabata, sai kuzarinsa ya riƙa raguwa sosai, kamar marasa laka a jikin. Ko mene ne yake faruwa a gare shi? Bari mu bi Hadiza zuwa cikin dajin can domin sanin abin da yake wakana.

**Fitowa ta 2: A gonar Mariya cikin daji**
Sama'ila, Hadiza

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Mhmmm, mhmmm, … |
| **HADIZA** | Sama'ila? Sama'ila? Kana ina ne, Sama'ila? |
| **SAMA'ILA** | Mhmmm. Ga…ga…ga ni nan. Kar ki ƙaraso inda nake, Hadiza, ki tsaya daga nan! |
| **HADIZA** | Ka fito daga inda kake. Me ya sa ka daina gudu, kowa ya damu. Ka fito mana, Sama'ila! |
| **SAMA'ILA** | Kada ki zo kusa da ni. Na ce ki koma! |
| **HADIZA** | Me ya sa ka daina gudun? |

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Ba daina gudu na yi ba. Cikina ne ya ruɗe. |
| **HADIZA** | Haba Sama'ila, kar ka zama sakarai. Ka daina gudun kuma ka kauce daga filin, ka faɗa daji. Ka fito daga wurin nan yanzu-yanzu, Sama'ila, ka fito! |
| **SAMA'ILA** | Ba zan iya ba, Hadiza. Kafafuwana sun gaza, saboda cikina ya ruɗe. Kar ki ƙaraso, kar ki shigo inda nake! |
| **HADIZA** | Kaiiiii!!! La la la! Wannan wane irin wari ne? Mmmm! Me ya mutu a nan wurin? Kai! |
| **SAMA'ILA** | Taki nake zuba a nan lambun mahaifiyarki. |
| **HADIZA** | Sama'ila, gudawa ta sake kama ka ne? |
| **SAMA'ILA** | Mhmmm… Kai! Mhmmm… |

**MAI BA DA LABARI:**
Assha, Sama'ilanmu yana cikin garari. Abin kunya ne ƙwarai. Budurwar da Sama'ila yake son burgewa a ko da yaushe, ta same shi a cikin wannan mawuyacin hali. Kaicon Sama'ila! Yaya Sama'ila ya kamu da wannan cuta? Ko akwai wasu 'yan zuriyar Sama'ila da su ma suka kamu da ita? Bari mu bi shi zuwa gida domin samun ƙarin bayani.

**Fitowa ta 3: A gidan Bilkisu**
Bilkisu, Mariya, Sama'ila

| | |
|---|---|
| **BILKISU** | O-ni-'yasu, yanzu yaya zan yi, Mariya? Ba ni shawara! 'Yata tana gudawa kamar ruwa. Me yake faruwa ne haka? |
| **MARIYA** | Bilkisu, na sha faɗa miki, ki riƙa dama wa Fati kamu mai kauri, zai taimaka mata wajen ɗaure mata ciki. Bari in je in dama kamu ki gani. Wannan zai yi maganin gudawar. Kuma ki faɗa wa ɗanki, ya daina yi mini bayan-gida a lambuna! |

**BILKISU** Sama'ila, don Allah, zo ka taimaka mini da yarinyar nan! Ungo ta, ni kuma in …

**SAMA'ILA** Kash! Don Allah, duba abin da Fati ta yi mini. Ta ɓata mini jikina.

**BILKISU** Ai ƙanwarka ce. Ko da ɗan ɓata maka jiki ai ba matsala. Ai kuma ba wannan shi ne karon farko ta take ɓata maka jiki ba. Ungo wannan ƙyallen, ka goge jikinka, sannan ka jefa shi can ƙuryar.

**MAI BA DA LABARI:**

Tirƙashi, ga dukkan alamu cutar gudawa ta samu gindin zama a wannan gidan! Akwai gudawa kaca-kaca a jiki da kuma kayayyakin mutanen gida. Kuma suna cikin ɗakin dafa abinci. Hakan ba ya da kyau. Ko hakan zai iya zama dalilin da ya sa cutar gudawan take ci gaba da yaɗuwa a cikin wannan gida? Cikin rashin sani, wannan gidan iyali zai ci gaba da yaɗa wa juna cutar, da kuma mutanen da ke kusa da su. Amma kuma yaya batun jaririyar nan Fati?

**Fitowa ta 4: A gidan Bilkisu**

Mariya, Hadiza, Sama'ila, Bilkisu

**MARIYA** Hadiza, ajiye kamun nan a can. … Kai Sama'ila, me ya sa kake riƙe yarinya haka, sai ka ce wani ɗaurin ayaba? Riƙo mini ita nan domin in ba ta kamun.

**HADIZA** Mama, na faɗa miki ba kamun Fati take buƙata ba, wurin likita ya kamata ki kai ta.

**MARIYA** Ka ji ki ko! Me kika sani dangane da ruɗewar ciki kina 'yar shekara 15? … Sama'ila, riƙo mini ita mana!

**SAMA'ILA** Hankali, ba ta da … ayya!

**MARIYA** Don Allah! Dubi abin da ka yi yanzu! Warin sai ka ce ɓeran da ya rage.

**BILKISU** Kakata takan ce, idan jinjiri ya yi maka haka, albarka ce.

**MARIYA** Tawa kakar ta yi amfani da ruwa mai tsarki ne, amma ba kashin jinjiri ba. Hadiza, za ki kawo kamun can ko a'a?

**HADIZA** Dakata, dakata!

**MARIYA da BILKISU** Mene ne?

**HADIZA** Ba ki wanke hannunki ba!

**MARIYA** Saboda me? Ai ba gawayi nake taɓawa ba.

**BILKISU** Hadiza, kina jin muna da ruwa mai yawa da za mu ɓarnata, mu yi ta wanke hannuwanmu ko da yaushe?

**HADIZA** Fati tana fama da gudawa, kuma malama ta ce, dole mu riƙa wanke hannuwanmu a ko da yaushe domin kada mu kamu.

**MARIYA** Rufe mini baki, yarinya! Wannan jinjira ce fa kawai, ba wata masana'antar fid da guba ba. Za mu ba ta abinci ko a'a?

**BILKISU** Yanzu kuma mene ne?

**SAMA'ILA** Wayyo Allahna! Tafiyar dole ta kama ni.

**HADIZA** Cikinshi ne ya ƙara ruɗewa.

**MARIYA** Tun da haka ne, shi ma yana buƙatar kamu mai kauri. Hadiza, maza tafi gidanmu, ki je ki ƙara yin wani kamun.

**HADIZA** Ina jin akwai buƙatar dukaninsu, su tafi asibiti. Hakan Malama ta ce….

**MARIYA** Rufe mana baki don Allah! Malama ta ce wannan, malama ta ce wancan. Wancan yaron da kike gani malalaci ne. Kun lura da yadda a cikin 'yan kwanakin nan yake zama kawai, ba ya yin wani abu? Ba ya ma sha'awar ƙara yin gudu kwata-kwata.

| | |
|---|---|
| **BILKISU** | Mariya, ke ƙawata ce, amma kuma ina jin cewa abin da kike yi wa ɗana bai dace ba. Ki ƙyale shi, ya sarara. Ki gode mana! A cikin 'yan makwanni biyun nan, ba taki yake zubawa a gonar taki ba? Kuma ma kyauta. |
| **MARIYA** | Idan takin gargajiya nake so kuma kyauta, ina samu ne daga kashin shanuna, amma ba daga wajen ɗanki malalaci ba, Bilkisu! |
| **BILKISU** | Ai dai kyauta ne, ko? |
| **MARIYA** | Yana da wari, kuma duk ya ɓata mini kayan lambuna. Ni ban ma ga abin da Hadiza ta gani a wajen Sama'ila ba, har take begenshi. A taƙaice, yarinya, na haramta miki hulɗa da yaron da ba ya iya riƙe cikinsa. Wa ya san abin da zai iya riƙewa. |
| **BILKISU** | Mariya, shin za ki taimaka mini da rashin lafiyar 'ya'yana ne, ko kuwa kin ƙudiri niyyar ƙara mini takaici ne? |
| **MARIYA** | Haba Bilkisu, yi haƙuri mana! Kin san fa wannan bakin nawa. … Fati ta yi tsit. Barci ne ya ɗauke ta? Kuma har yanzu ba ta sha kamunta ba. |
| **BILKISU** | Takan yi haka. Tana fama da gudawa, ta yi ta kuka, idan ta gaji, sai ta yi barci. Idan ta farka kuma ta ci gaba da kukan. Ta ma daina cin abinci sosai. |
| **MARIYA** | Ga alama launin jikinta ya canja. Yanzu tana kama da wani busasshen ganye! |
| **HADIZA** | Malamarmu ta shaida mana cewa ƙazanta ke janyo cutar gudawa. |
| **BILKISU** | Yarinya, me kike nufi? Kina nufin gidana yana da ƙazanta? |
| **MARIYA** | Bilkisu, kada ki ƙara yi wa 'yata tsawa. Tana faɗin abin da malaminta ne kawai ya ce. |

**HADIZA** Malamarmu ta ce mutanen da suke fama da cutar gudawa, suna zub da dukkan ruwan da suka kamata su zauna a cikin jikinsu.

**MARIYA** Tsaya. Tsaya, Hadiza! Yaushe kika ƙara zama mai basira haka? A ko da yaushe za mu iya samun magani daga ƙananan shaguna.

**HADIZA** Ta ce dukkan wanda yake son zuwa banɗaki domin biyan buƙata, amma kuma zai je wurin fiye da sau huɗu a rana, akwai buƙatar ya ga likita…

**MARIYA** 'Yammata, kin fa fara ɓata mini rai!

**BILKISU** Zai yiwu akwai buƙatar mu nemi shawarwari daga surukina Adamu da kuma matarsa Likita Husaina. Kin gane ai domin kada mu yi sakaci.

**MARIYA** A'aha! Ai kuma sai ki yi!

**MAI GABATARWA:**

Shakka babu, gidan su Bilkisu yana cikin ƙunci. 'Ya'yanta ba su da lafiya, ga shi kuma Hadiza wadda ga alama ta fahimci mummunan halin da suke ciki, ba a sauraren shawarwarinta. Masu sauraronmu, yau a nan za mu dasa aya a cikin wannan shiri. Sai kuma a mako na gaba in Allah ya kai mu inda za ku ji ci gabanshi. Kafin nan kuna iya sauraronmu a adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.